MINISTÈRE
DE L'EUROPE
ET DES AFFAIRES
ÉTRANGÈRES
*Liberté*
*Égalité*
*Fraternité*

DIRECTION DES RESSOURCES HUMAINES
———
SOUS-DIRECTION DE L'ATTRACTIVITÉ ET DES RECRUTEMENTS
———
Bureau des concours et examens professionnels

# Concours externe et interne pour l'accès à l'emploi de secrétaire des affaires étrangères (cadre d'Orient) au titre de l'année 2025

## Épreuve écrite d'admissibilité

26 septembre 2024

# Haoussa

Durée totale de l'épreuve : 3 heures – coefficient 2
*Toute note inférieure à 10 sur 20 est éliminatoire.*
***Barème** : composition en haoussa 12 points ; traduction en français 8 points.*
Dictionnaire autorisé

## Composition

Composition en haoussa à partir d'une question rédigée dans cette même langue, liée à l'actualité
**(350 mots avec une tolérance de plus ou moins 10%)**

## Sujet

A ganinku, yanzun da 'yan-Adam suka ƙaru a duniya, kuma ga kuɗin mai na ƙaruwa, waɗanne dabaru za a iya yi don a rika samun isasshen amfanin gona ga jama'a ? Ku ba da misalan da za ku ɗebo daga ƙasashe daban-daban.

MINISTÈRE
DE L'EUROPE
ET DES AFFAIRES
ÉTRANGÈRES

*Liberté*
*Égalité*
*Fraternité*

DIRECTION DES RESSOURCES HUMAINES
———
SOUS-DIRECTION DE L'ATTRACTIVITÉ ET DES RECRUTEMENTS
———
Bureau des concours et examens professionnels

# Concours externe et interne pour l'accès à l'emploi de secrétaire des affaires étrangères (cadre d'Orient) au titre de l'année 2025

**Épreuve écrite d'admissibilité**

26 septembre 2024

## Haoussa

Durée totale de l'épreuve : 3 heures – coefficient 2
*Toute note inférieure à 10 sur 20 est éliminatoire.*
***Barème** : composition en haoussa 12 points ; traduction en français 8 points.*
Dictionnaire autorisé

### Traduction

Traduction en français d'un texte rédigé en haoussa

**Texte au verso**

## Renon ƙasa

In ƙasar gona ta lalace, wajibi ne ga manomi ya sami hanyar gyara. Ta noman da yake yi, yana ɗauke wa ƙasa arzikinta, saboda haka wajibi ne ya mayar mata.

Akwai abubuwa waɗanda dukan tsire-tsire suke buƙata su samu daga ƙasa. Ka sani, in ka ƙona itace ko ciyawa, za su koma toka. In ka lasa tokar, za ka ji ta yi kanwa-kanwa. Ka ga ita wannan kanwa-kanwa ashe da ma tana cikin itacen, kuma da fari shi itace ya same ta daga cikin ƙasa ne. Kanwar da ka ɗanɗana ba iri ɗaya ba ce, abubuwa ne kamar uku suka taru suka yi ta. Amma dukansu ya kamata a same su cikin ƙasar gona, in dai ana so shuke-shuke da za a yi cikinta su yi kyau.

A waɗansu wurare, al'adar manoma in sun ga gonarsu ta shure, sai su bar ta su sake sarar wata, su sare itatuwa su ƙone daji. Ƙonawan nan ɓarna ce, amma manomi ba zai ga haka ba. A shekara ta farko, ƙila har da ta biyu, zai ga ya sami amfanin gona mai yawa. Tokar dajin da ya ƙona ta zame masa taki. Amma duk da haka takin nan da yake samu ba duka zai tsaya masa ba. Iska da ruwa sukan ɗauki tokar su tafi da ita. Ka ga ashe da bai ƙone ba, da sai hakukuwa su ruɓe, kanwa-kanwar da ke cikinsu duka ta sake komowa cikin ƙasa. Ta haka sai ya daɗe yana noman gonarsa, ba ta shure ba.

A zamanin da, sa'ad da akwai daji farara a ko ina, ko manomi ya ɓata wannan gona, sai ya karkata ya sari sabuwa. Amma yanzu, da mutane suka ƙara yawa, a waɗansu wurare sai ka ga ƙasar noma ta yi musu kaɗan. Dole kowa ya yi ƙoƙari ya riƙe gonarsu ta gado. Yanzu ba daidai ba ne ya bar gonarsa ta lalace, ya je ya sare daji barkatai. Wanda ya yi haka ya yi wa 'ya'yansa da jikokinsa laifi. Da zai dawo duniya a lokacinsu, da sun yi shari'a da shi.

Manoma sun gane, in kana ta shuka irin abu guda a bisa gona, sai ka ga abin da ka samu bana bai kai na bara ba, na bara bai kai na bara waccan ba. Amma in kana sake irin abin da za ka shuka, sai ka ga, ko ba ka zuba taki, gonar ta yi shekara kamar uku ba ta sallace ba. Dalili, shuke-shuke duk suna buƙatar abinci daga ƙasa, amma su duka ba abinci iri ɗaya suke buƙata ba. Mun ce kanwa-kanwar nan da ke cikin ƙasa, waɗanda shuke-shuke ke ci, ba iri ɗaya ba ne. Shuke-shuke suna buƙatarsu duka, amma kowace shuka akwai irin kanwar da ta fi buƙata. Saboda haka, in wannan shuka ta ci irin kanwar da take buƙata da yawa a ƙasa, sai ka ga ta bar irin wadda ba ta buƙata, don wata shukar mai son irinta.

Takin da aka samu daga wurin dabbobi, shi ma yana da irin kanwan nan da shuke-shuke suke buƙata ƙwarai. A ƙasashen arewa, inda babu ruwan sama mai yawa, manoma sun saba da sa irin wannan taki a gonakinsu. Tilas ne su yi amfani da shi. Inda akwai mutane da yawa, kamar karkara ta kusa da manyan birane, manomi ba shi da wani sabon daji da zai sare ya yi gona, kome himmarsa. Tilas ya zauna bisa gonarsu ta gado, ya yi ta shuka a bisanta kowace shekara.

Kowace shekara, in damina ta kusa, sai ka ga mai gida yana ta kwaso share-sharen gida da kashin dabbobi wanda ya tara, yana kaiwa gona.

Dabara ce ma mutum ya umurci mutanen gidansa su riƙa zuba shara cikin ɗakin awaki, don ta cuɗanya da kashinsu, kuma ta haka ba za ta bi iska ba. Amma duk dabarar da ta fi, ka yi rami mai faɗi amma ba mai zurfi ƙwarai ba. Ciki za ka ce a yi ta zuba sharar gida, watau ciyayi da ganyaye da kara da toka, da ɓawon su doya da dankali da rogo, har da kashin dabbobi. Kowane abu da zai iya ruɓewa taki ne. In ka ga an tara shara da dama, cuɗanye da kashin dabbobi, sai ka samo 'yar ƙasa ka rufe su, a ci gaba kuma da zubawa. In ya sake taruwa, ka sake sa 'yar ƙasa ka rufe, a ci gaba. Ka yi ƙoƙari kuma ka riƙa yayyafa ruwa a bisa, amma kar ka zuba da yawa. Bayan mako biyu ko uku, sai ka shiga ka juya. Abin da ya taru a ramin nan zai yi zafi ya ruɓe da sauri. Zafin nan yakan kashe ƙwayoyin ciyayin waɗanda ba su da amfani, yakan kuma kashe ƙwayayen ƙudaje da ƙwari. A ƙarshen rani, in an fara ɗibar taki za a kai shi gona, sai ka ga duk abin da ke ciki ya ruɓe. Wannan shi ne taki wanda ya fi kowane kyau.

***Source*** *: Ikon Allah – Duniya sama da ƙasa, Abubakar Imam, 1966, Zaria, Northern Nigerian Publishing Company, pp. 60-63*